Ka bar abinda kake kokwantansa zuwa abinda baka kokwantansa, domin gaskiya nutsuwa ce, kuma ƙarya kokwanto ce

Daga Abul Haura'u al-Sa'adi ya ce: Na cewa Hassan ɗan Ali - Allah Ya yarda da su -: Me ka haddace daga Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -? ya ce: Na haddace daga Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: "Ka bar abinda kake kokwantansa zuwa abinda baka kokwantansa, domin gaskiya nutsuwa ce, kuma ƙarya kokwanto ce".

[Ingantacce ne] [Tirmizi da Nasa'i da Ahmad ne Suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi umarni da barin abinda kake kowanto a cikinsa na maganganu da ayyuka cewa shi an hana ne koko a'a, shin shi haramun ne ko halal ne, zuwa abinda babu kokwanto a cikinsa daga abinda ka sakankance kyansa da kuma halaccinsa, domin cewa zuciya zata nutsu gare shi ta samu kwanciyar hankali, abinda kuma a cikinsa akwai kokwanto to zuciya tana kaikawo daga gareshi kuma tana raurawa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/4564